Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.3 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Kyauta A Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Aminu A. Ibrahim,**
**Abubakar Ɗanillela**

Sashen Hausa na Kwalejin Ilimi, Shehu Shagari Sokoto

**Corresponding Author: Aminu A. Ibrahim** uaibrahim7@gmail.com
**Lambar waya : 08062716148**

**Tsakure**
Hausawa kan ce "Yaba kyauta tukuici" kyauta wata ɗabi'a ce mai kyau wadda ake girmama mai yinta da sonsa cikin al'umma. Wannan maƙala ta dubi waƙoƙin makaɗa Kassu Zurmi domin tsakulo ire-iren kyautukan da yake bayyanawa a cikin waƙoƙin da yake yi wa gwarazansa. Wannan maƙalar ta bayyana hikimar Kassu Zurmi wajen bayyana kyautar da yake samu ga Gwarazansa domin ya bayyanasu ba marowata ba ne. Wannan maƙalar ta bi ra'in Gusau (1983) in da ya yi amfani da shi kan nazarin waƙar baka Bahaushiya musamman wadda ta yi bayani dangane da adabin baka da maganganun hikima. Haka kuma wannan maƙalar ta bi hanyar sauraren waƙoƙin Kassu cikin kaset-kaset da kuma waɗanda ta samo daga da littafin da magaji (2016) ya rubuta da kundin digiri na biyu na Habib Kaura (2017) wajen samun waɗanna waƙoƙin.

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.1 Gabatarwa

Manazarta da dama sunbayyana mawaƙan baka da cewa ba kaji ba ne. Ayuba (2013) da Ibrahim (2015) duk sun bayyana haka. Duk mawaƙan ƙasar Hausa idan aka yi masu kyauta su kan bayyana an yi masu domin su yi godiya ga waɗanda suka yi masukyauta. Makaɗan maza ma suna cikin waɗanda ke bayyana wannan. Kassu Zurmi yana bayyana an yi masa kyauta da yadda kyautar ta samu ko da, da tsiya aka sami kyautar.

Wannan maƙalar ta dubi waƙoƙin makaɗa Kassu Zurmi domin fito da ɗiyan waƙar da ke ɗauke da wannan kyautar da aka yi masa. Bayan da aka dubi taƙaitaccen tarihin Kassu da ma'anar kyauta da ire-irenta daga ƙarshe za a kawo sakamakon bincike sai kammalawa.

## 1.2 Taƙaitaccen Tarihin Makaɗi

Makaɗa Kassu Zurmi sunansa na asali Abubakar Ɗan Muhammadu Ɗan Ganɗau. Bagobiri ne daga Kurawa ta ƙasar Gobir suka yaɗa zango a garin Dunfawa da ke ƙaramar hukumar mulkin Zurmi ta Jahar Zamfara ta yanzu Ganɗau ya taɓa zama Sarkin Fawan Dunfawa. A nan aka haifi Muhammadu mahaifin Kassu. Muhammadu yana yin kiɗa na farauta. Bayan wasu shekaru yawon kiɗa ya kai shi garin Magarya sai ya zauna nan da iyalansa har zuwa lokacin da aka haifi Abubakar Kassu.

Mahaifiyar Kassu kuma ana kiranta da Maimuna, amma an fi sanin ta da sunan Kande (laƙabin da ake yi wa wadda da aka haifa bayan haihuwar maza). To Kande dai Bazamfara ce mutumniyar Magarya ce a nan ne mahaifin Kassu ya ganta ya aure ta lokacin da suka taso daga Dunfawa suka koma Magarya.

An haifi Alhaji Abubakar Kassu Zurmi a garin Kadawa ta cikin ƙasar Zurmi a ƙaramar hukumar mulkin Zurmi ta Jahar Zamfara. Nisan ƙauyen da garin Magarya kilomita biyu ne kawai. An haifi Kassu ranar Laraba wadda ta yi daidai da ranar kasuwar Dunfawa a shekarar 1910 wannan ya sa aka sa masa laƙabin Kassu (gajarta sunan kasuwa) (Kaura, 2017).

Gusau (2005) ya bayyana makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya fara kiɗan noma bayan koyan kiɗan da ya yi ga mahaifinsa, amma bai mai da hankalinsa sosai ba. Ya maida hankalinsa ne ga kiɗan farauta da ya gada daga mahaifinsa har ya sami rabo mai yawa ciki.

Kassu ya zamo yana yin kiɗansa har cikin dazukan da ake yin farauta domin gwarzantar da Ubannin gidansa kuma ya zuwa gidajensu ko kuma idan aka gayyace shi wani biki. Kassu ya shahara wajen kiɗan maza wato 'yan tauri da mafarauta, da kuma wani lokaci ɓarayi wadda ba sosai yake yi masu waƙa ba. Gusau (2005) ya bayyana sarkin Zamfara Zurmi ya naɗa Kassu Sarki kiɗan Maza da ƙasar Zurmi.

Kassu na da iyali da dama. Allah ya azurta shi ɗiya maza da mata masu yawa. Kassu Zurmi ya rasu bayan wata rashin lafiya da ya yi harya kwanta asibitin Gwamnati ta Gusau a 1987. Allah ya gafarta masa Amin.

## 2.0 Ma'anar Kyauta

Kyauta na nufin bayar da wani abu daga abin da Allah ya hore wa mutum ga wani mutum ba da nufin a biya shi ba. Kyauta kuwa dangane da mawaƙa ta dogara ne ga irin dangantakar da ke tsakanin mawaƙi da wanda yake yi wa waƙa. idan mawaƙi ya ƙware wajen tsara waƙa ta hanyar zaɓen daɗaɗɗau kalmomi da saƙa su cikin azanci domin burgewa, to akwai yiwuwar ya sanin kyauta mai yawa daga wanda ake yiwa waƙar ko makunsantansa ko masoyansa.

## 2.1 Ire-iren Kyauta

Duk wani abu da yake da muhimmanci Hausawa sukan yi shi kashi-kashi i. kyautar ƙasaita ii. kyautar tilas iii. kyauta biyan bukata.

### 2.1.1 Kyautar Isa (Kasaita)

Kyautar isa kyauta ce da wanda aka yi wa ita zai kasa yin godiya ha-sa-lima yana iya fashewa da dariya ko kuka za a gan shi kamar ya zautu. Kassu ya nuna an yi masa irin wannan kyautar cikin waƙar da ya yi wa sale na Gidan goga. Indayake cewa:

Sai nij ji sallama

Giwa ta darkako
Jin kau nikal bicit
Jin kau nikal bicit
Kaya ɗai ga jiɗa
Ji kan nikai titib
Jin ɗai nikai titib
Na Amadu gogan dare ina ɗaka.
Na ji sallama nih hito
Nay yi tuntuɓe da dila
Ta kai zuwa cikina
Nid dawo
Nay yin an haka,
Kuma nai tuntuɓe da ƙunshi
Ya kai ga nan gatona
Kuma nid dawo
Nik koma gaɗau-gaɗau nan niya
Niy yi tuntuɓe da dila
Ta kai zuwa guwawuna
Nic ce Bahago mi a haka kashi-kashi
(Kassu: Waƙar Sale na Gidan goga).

A cikin wannan ɗan waƙa Kassu ya nuna kyautar da salen Gidan goga ya yi masa ba 'yar ƙaramar kyauta ba ce domin ya yi amfani da kalmar da ke nuni da haka wato kalmomin bicit da titib duk kalmomin ne masu nuni da abu mai yawa ne aka sauke da yanayin faɗuwar su.

### 2.1.2 Kyautar Tilas

Kyautar tilas kamar yadda sunanta ya nuna kyauta ce wadda mai yinta ya yi ta ne ba don son rayuwarsa ba domin kawai an tilasta shi ne ya yi ta. Kassu Zurmi ya yi wa Sabatacce inda yake cewa:

Tsaya a raba ƙwazo na Mande
Tsaya a raba
Cilas anka raba shi biyu
Rannan garugaru yay mani daɗi
Ɗan sanda kamar na dama zuma na sha
(Kassu: Waƙar Sabatacce).

A cikin wannan ɗan waƙa za a gano cewa Kassu ya bayyana inda aka sa a yi masa kyautar tilas domin an yi gumurzun faɗa wanda Kassu ya lissafa mazajensa da yawa waɗanda suka kasa zuwa amsar wannan kwaron da ake kira Dunguzu. Sai da Sabatacce ya zo ya nemi ya amshoshi sai waɗanda yake hannunsu su gano za su yi biyu babu wato ba su ga tsuntsu ba su ga tarko don haka sai suka fara neman sulhu da Sabatacce wanda ya ce ko dai su bada Dunguzu ko kuma a raba shi biyu su ɗau rabi a ba Kassu rabi suka yarda bisa ga tilas ba don sun so ba.

## 3.1 Kyauta a Cikin Waƙoƙin Kassu

Kamar kowane makiɗin da ke ƙasar Hausa yake ambatar abin da Ubangidansa ya ba shi kyauta. To Kassu Zurmi yana cikinsu domin yana nuna duk abinda ya samu ga waɗanda yake yi wa waƙa suka ba shi ko da ko abin ba mai cika fuska ba ne. Kyauta a cikin waƙoƙin maza ba kamar kyautar sarakuna da Attajirai ba ce kyauta ce wadda take daidai ƙurji

daidai ruwansa wato kamar kumbo kamar kayanta. Kassu yana bayyana kyautar abu mai yawa da ɗan kaɗan misali a cikin waƙar Shaho Kassu yana cewa:

Na goje bai gama kyauta ba,
Ba ni sanyi da kiɗi nai
Ya ba ni doki ya ban alkyabba
Ya ban kufta
Shaho kuma yab ban aska takwas ta saƙI ta Nufe
Yai mani matad da anka wankam ma na idda.
(Kassu: Waƙar Shaho).

Idan aka dubi wannan ɗan waƙa za a gano cewa Kassu ya yi amfani da salon ƙirge wajen bayyana kyautar da Ubangidansa ya ba shi waɗanda sun haɗa doki, da alkyabba da kufta da riga aska takwas ta saƙi ga ƙarshe ya nuna ya aura masa mata. Duk waɗannan abubuwa da Kassu ya lissafa suna, bayyana wannan kyautar babba ce kamar wadda Ibrahim (2015) ya bayyana cewa amfani da ƙirge wajen lissafa abin da Ubangidan makaɗi ya bayar kyauta yana nuna wannan kyautar babba ce. A cikin waƙar da Kassu ya yiwa Muhammadu Na Sale ya bayyana irin kyautar da ya yi masa inda yake cewa:

Bautag godiya ga Mamman Dan Sale
Doki takwas ya baya
Amma hwa hay yau kari ne yay yi man
Ba biyan taki ba
Wanda nike so kay yi man Mamman mai geza.
(Kassu: Waƙar Mamman Dan Sale).

Idan aka dubi wannan ɗan waƙa za a ga cewa makaɗa Kassu ya bayyana kyautar da wanda yake yi wa kiɗa ya ba shi har dawaki takwas kuma ya ƙara masa na yayi irin wanda yake so ne ya bashi. Idan aka duba ta wata fuskar za a ga cewa wannan kyautar ma babba ce domin ga ɗan tauri kyauta da doki ɗaya ma abu ne mai wuya domin tsiya ce taƙamarsa ba arziki ba amma ya ba shi har dawaki takwas. A cikin wata waƙa da ya yiwa Basare na Gwamma Kassu ya bayyana irin kyautar da ya samu inda yake cewa:

Basare yac ce Kassu duk shekara
Ka dawo imma doki
Na koma ya ba ni
Kuma nik koma yaƙ ƙara
(Kassu: Basare na Gwamma)

Idan aka dubi wannan ɗan waƙa za a ga makaɗa Kassu ya bayyana ya yi wa Basare kiɗa ne shi kuma ya yi wa Kassu alkawalin cewa ya zo shekara mai zuwa zai masa doki. Kassu ya bayyana da shekara ta cika ya zo wajen Basare kuma ya ba shi doki kuma wata shekara ta zo ya ƙara masa wani dokin. Wannan kyautar ita ma babba ce domin ya yi amfani da salon ƙirge domin shekara biyu ana ba shi kyautar doki ba doki guda aka bayar ba a kowace shekara an bashi doki kamar wadda ya bayyana cikin wannan ɗan waƙar. A cikin waƙar da ya yi wa Na gidan Duwa Kassu ya bayyana irin kyautar da ya samu inda yake cewa:

Mai dabo jikan baya, ka biya
Doki kas sai mani
Gajere mazaizan duniya
Na gode na gidan Duwa
Ka yi man komi
Na gode na gidan Duwa
Ka yi man komi

(Kassu: Na gidan Duwa)

A cikin wannan ɗan waƙa za a ga makaɗa Kassu yana bada labarin cewa Na gidan Duwa ya biya shi kiɗin da ya yi masa domin ya sai doki ya ba shi kyauta wannan kyautar ita ce ta haifar da wannan yabon na nuna shi da cewa su ne mazajen Duniya waɗanda ake yi dasu ta fuskar jarunta. Karshe kuma ya yi masa godiya.

A cikin wata waƙa da ya yi wa Sabatacce ya bayyana kyautar da ya samu inda yake cewa:

: : : : :

Tsaya a raba ƙwazo Na Mande
Tsaya a raba
Cilas anka raba shi biyu
Ranan Garugaru yay mani daɗi
Dan Sanda kamar na dama zuma na sha.
(Kassu: Waƙar Sabatacce).

Makaɗa Kassu Zurmi ya bayyana }wazo Sabatacce ya sa an yi masa kyauta wadda ya tilasta wanda ya kama ƙunzugu ya raba shi biyu aka ba Kassu rabi shi kuma Sabatacce ya ce da Kassu ya ɗauka. Kuma wannan kyautar ta samu ne ta hanyar irin zaruntar wanda ake yi wa kiɗa ya nuna domin can farko Kassu ya bayyana ya kawo wasu mafarauta sun kasa ɗibar masa komai daga hannun waɗancan da ƙunzugun yake hannunsu sai da shi Sabatacce ya zo Kassu ya zuga shi ya faɗa masu kuma ya sami nasara ya riƙi ƙunzugun, ganin haka ne yasa suka ga za su yi biyu babu suka cewa Sabatacce ya yi hanƙuri a raba shi biyu, ya kuma yi hanƙurin aka raba biyu aka baiwa Kassu rabi. Shi ne Kassu ka faɗin abin ya yi masa daɗi ya ji kamar ya dama zuma ya sha. Wannan kyautar ƙarama ce domin abin da aka samu kyauta ƙaramin abu ne.

A cikin wata waƙa da ya yi wa Maishibra Kassu ya bayyana kyautar da yake samu wajen Maishibra da cewa:

Na labbo kai mani kyauta ina gida zamne na
- - - - - - - -
Ba lotton da ba ka yi man kyauta ba
Iro uban Nasake Na Labbo Ɗan namijin Duniya.
(Kassu: Waƙar Maishibra).

A cikin wannan ɗan waƙa makaɗa Kassu ya bayyana kyautar da Maishibra yake masa ta koyaushe wato yana yi masa kyauta in sun haɗu, kuma yana aika masa da abin da ya samu gida inba su haɗu ba. Kuma wannan kyautar ita ce ta haifar da wannan yabo na kiransa da Namijin duniya wato gwarzo ne ga harkokinsa. Wannan kyautar ƙarama ce domin makaɗa bai bayyana abin da aka ba shi kyautar ba kamar wadda Ibrahim (2015) ya bayyana cewa rashin ambaton abin kyauta ya nuna cewa wnanan kyautar ƙarama ce.

## 3.2 Sakamakon Bincike

Wannan binciken ya gano wasu abubuwa da dama kamar haka:

1- Binciken ya gano cewa: Ba makaɗan fada ko na jama'a ke samun kyautar kirki ba suma makaɗan maza suna samun kyautar gwargwado amma ba kamar yadda su makaɗan fada suke samu ba.
2- Binciken ya gano yadda makaɗan fada suke zuga ubangidansu ya yi masu kyauta su ma makaɗan maza haka suke, sukan zuga gwarazansu domin neman kyauta
3- Binciken ya ganocewa makaɗan maza layinsu ɗaya da makaɗan fada domin jigoginsu na ƙawancen juna sai dai kowa da nasa.Ta fuskar yabo da zuga da zambo

da habaici da roƙo.Sai dai shi sarki ana yabonsa ne ta hanyar bayyana halinsa da nasabarsa da zaruntarsa da sauran halaye nagari. A ya yin da kuwa 'yan tauri da makantansu ana yabonsu ne da akasin waɗannan halaye.

4- Binciken ya gano makaɗan maza sukan bi waɗanda suke yi wa kiɗa har daji domin ƙara zuga su don su ƙara jajircewa ga abinda suka je yi.

5- Binciken ya gano makaɗa Kassu Zurmi, makaɗi ne da yake yiwa 'yan tauri da mafarauta wani lokaci kuma yakan yi |arayi waƙa.

## 4.0 Kammalawa

Hausawa na cewa "laifin daɗi ƙarewa" ko "komi nisan jifa ƙasa ta yo". Nan ƙarshen wannan bincike wanda ka yi akan kyauta a cikin waƙoƙin Kassu Zurmi inda aka yi gabatarwa da bayar da ɗan taƙaitaccen tarihin makaɗa Abubakar Kassu Zurmi.An bayyana shi Bagobiri ne wanda aka haifa a garin Magarya ta ƙaramar hukumar mulkin Zurmi ta jahar Zamfara. Bayan haka an bayyana ma'anar kyauta da ire-iren kyauta da kuma kyauta a cikin waƙoƙin Abubakar Kassu Zurmi da bayyana ma'auninsu na babbar kyauta da ƙarama sai sakamakon bincike inda aka bayyana abubuwan da bincike ya gano.

## Manazarta


Abba, M & Zulyadaini B. (2000). *Nazari Kan Waƙar Baka ta Hausa* Zariya. Gaskiya Corporation Ltd.

Ayuba A. (2013) kyantayin Bahaushe A Waƙoƙin Baka. Kundin Digiri Na biyu. Zari'a Jami'ar Ahmadu Bello

Bargery. GP. (1993) *A Hausa- Engulish Dictionry and English- Hausa Vocabulary* 2nd Edition Zari'a Ahmadu Bello University Pree Limited

Dunfawa, A.A. (2013) Gambo A Zubin Mawaƙan Baka. Cikin Mujallar Makaɗi A Mahangar Manazarta. Sokoto Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo

Gusau, S.M. (2005). *Makaɗa da Mawaƙan Hausa.* Kano Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2009). *Dirwanin Waƙoƙin Baka:* Zaɓaɓɓun Matanoni na Waƙoƙin Baka na Hausa. Kano Century Research and Publishing Ltd.

Gusau S M (2008). *Waƙoƙin Baka na Kasar Hausa.* Kano benchmark Publishers Limited.

Ibrahim, A.A. (2015). Kyauta ma'aunin Yabo A Cikin Waƙoƙin Fada na Hausa. Sokoto Kundin Digiri na Biyu Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Kaura, H.L. (2017) Salon Zayyana (Hotancin Zuciya) A waƙoƙin

Kassu Zurmi. Sokoto Kundin Digiri na Biyu Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Magaji A (2016) *Kassu Zurmi Da Waƙoƙinsa*. Ibadan Spectium Book Limited

Yahya, A.B. (2001). *Salo Asirin Waƙa*. Kaduna. Fisbas Media Service Limited.

Zamfara, R.S. (2022). Salon Kambamawa A Cikin Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi. Cikin https//www.amsoshi.com.